# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Ni ma ɗan Adam ne: 'Yan Afirkan da ke fama da taɓin hankali
## Kashi na takwas: Canza halaye


| | |
|---|---|
| Wanda ya rubuta: | Chrispin Mwakideu |
| Wanda ya fassara: | Yusuf Idris |
| Wadda ta tace: | Halima C. Schmaling |


**'Yan Wasa:**

| | |
|---|---|
| Amina: | 'yar shekara 19 |
| Dije: | 'yar shekara 19 |
| Duduwa: | 'yar shekara 35 |
| Musa: | ɗan shekara 16 |
| Mandu: | ɗan shekara 40 |
| John: | ɗan shekara 25 |
| Patel: | ɗan shekara 40 |
| Kashiya: | 'yar shekara 20 |
| Mudi: | ɗan shekara 50 |

**Mai gabatarwa:**
Jama'a, barkanmu da sake kasancewa da ku a cikin kashi na takwas na shirinmu na "Ji Ka Karu" wanda muke kawo muku a kan mutane masu fama da cutar taɓin hankali a nahiyar Afirka. A cikin shirin da ya gabata kun ji yadda Duduwa ta kai ɗanta Musa wajen likita, wanda shi ne kaɗai ƙwararre a kan ciwon taɓin hankali a ƙasar baki ɗaya. Likitan yana ganin kamar cewa ciwon ƙwaƙwalwa ne da yake kama mutane tun suna ƙanana ya kama Musan. Sannan mamaki ya kama Dije a lokacin da ƙawarta Amina, wadda taɓin hankali ya same ta, ta dawo ɗakinta a makaranta bayan ta guje mata lokacin da ta gan ta a kan titi. Daga ƙarshe kuma, John ya nemi taimako a wajen ƙwararren likitan nan, Dr. Mudi, bayan ya gane cewa yana fuskantar barazana a kan lafiyarshi na zama cikin takaici. Bari kuma yanzu mu ji abin da zai faru a cikin wannan shiri mai taken "Canza halaye". Za mu faro shirin ne daga inda Amina da Dije ke cin abinci.

**Fitowa ta 1: A ɗakin Dije**

**Amina:** Na gode. Na gode, Dije. Na gode ƙwarai da gaske da kika ba ni kayanki na sa. Ban taɓa sanin cewa malamanmu sun sa an kwashe min duk wani abu nawa ba, kuma an adana min su.

**Dije:** Ai saboda dole a ba wata ɗalibar ɗakinki ne. Kin san ban taɓa faɗa wa shugabannin makarantarmu abin da ya same ki ba. Sai dai wasu daga cikin ƙawayenmu, ba kowa ne ya san halin da kike ciki ba.

**Amina:** To amma yanzu na dawo, kuma ina so in ci gaba da karatu na. Yanzu ba na jin komai.

**Dije:** Amina, ina ganin haka bai kamata ba tukuna. Yau da safe da kika zo kin zo ne a cikin wani mummunin hali. Na ji

daɗi da kika ce min ba kya jin komai yanzu, amma har na zuwa wane lokaci ne Amina? Awa ɗaya, kafin rana ta yi? Daga nan kuma sai a koma gidan jiya. Mu je mu ga likita. Na yarda in kasance tare da ke har wannan abin ya ƙyale ki. A shirye nake in taimake ki, amma sai ke ma kin nuna kina son taimakon.

**Amina:** Kwarai da gaske ina son taimakon. Ba na son in ƙara jin muryoyin da nake ji, kuma idan har wannan likitan zai taimake ni, me zai hana ni zuwa wurinshi, mu je. Na shirya.

**Dije:** To ya yi daidai. In tambaye ki wani abu, Amina. Idan kina jin muryoyin nan, me suke ce miki? Sannan kuma muryoyin na mata ne ko na maza?

**Amina:** Ni ma ban sani ba. Na san cewa dai ina fuskantar barazana ne. Kuma sai ina jin kamar waɗanda suke tare da ni su ma suna fuskantar barazanar.

**Dije:** Dalilin da ya sa kika guje min ke nan a daren da na gan ki a cikin gari?

**Amina:** Wataƙila, ban dai sani ba. An bar ni a baya sosai a makaranta?

**Dije:** Kwarai da gaske Amina, amma kar ki damu. Idan dai likitan ya duba ki kuma ya ce za ki iya ci gaba da karatunki, ai wannan ba wani abu ba ne. Kin shirya mu tafi?

**Amina:** Na shirya? Shirin me?

**Dije:** Wayyo Allahna! Na shiga uku, abin ya dawo…

**Mai ba da labari:**
Amsar ƙarshen da Amina ta bai wa Dije ya jefa ta cikin wani ruɗanin. Ita a tunaninta, ƙawarta ta warke! Ku ci gaba da sauraro don ku ji abin da zai faru nan gaba. Har ila yau a wannan garin dai, Duduwa ta faɗa wa yayanta Mandu cewa, ɗanta Musa na iya kasancewa da wannan cutar har iya ƙarshen rayuwarsa. Shi kuwa Mandu da yake cikakken mabiyin addinin Krista ne, ya yi amana da cewa yana da mafita game da abin da ɗan Adam ya kasa yi. Saboda haka sai a asirce ya gayyaci 'yan'uwanshi maza da mata da suke bauta tare a cocinsu don su yi addu'ar tsakar dare don su kori aljanun da suka kama ɗan kanwarshi, wato Musa.

**Fitowa ta 2: A gidan Mandu**

**Duduwa:** Yaya Mandu, bari in gan ka a gefe ɗaya mana.

**Mandu:** To shi ke nan, ina zuwa. 'Yan'uwa, ku ci gaba da yin addu'a da waƙa. Yau sai mun fi ƙarfin sheɗan da daddaren nan! Yau sai mun ƙwaci ɗana!

**Muryoyi:** Amen! Amen! Amen!

**Mandu:** Zan dawo yanzun nan.

**Duduwa:** Yaya Mandu, na ji daɗin abin da ka yi, amma me ya sa ba ka faɗa min cewa ka shirya a zo a yi addu'a ba? Musa ba ya son taron jama'a! Ba ya son ya ga mutane kawai sun faɗo mai. Na sha faɗa maka haka.

**Mandu:** Duduwa, wancan ba Musa ba ne. Shaiɗanun da ba sa so mu yi magana da yaron ne. Suna jin tsoron addu'a kuma ba sa so su sake shi. Dole ne mu taimaki Musa.

**Duduwa:** Amma Mandu, na faɗa maka cewa ƙwarrarren likitan ƙwaƙwalwan nan, Dr. Mudi, ya ce mu ba za mu iya warkar da Musa ba. Sai dai a yi ƙoƙarin inganta rayuwasa, amma ba wai ya warke kwata-kwata ba. Ciwon ƙwaƙwalwa ne ke damunsa.

**Mandu:** Haka ne, amma ki sani, addu'a na iya warkar da ciwon da ɗan Adam ba zai iya warkarwa ba. Ki yarda da mu ƙanwata, za mu kuɓutar da Musa daga aljanun da suke ta damunshi tun yana ƙarami.

**Duduwa:** Mandu, da ni ma ina irin wannan tunanin. Amma bayan da likitan ya yi min bayani sosai, ina ganin ya kamata mu gwada shawarar da ya bayar. Shi ne na koya wa Musa yadda zai riƙa canza halayenshi, sannan ni kuma a matsayin mahaifiyarsa, a koya min yadda zan riƙa kula da shi. Abin da za a yi ba zai warkar da shi ba, amma zai sa irin halayrn da yake shiga ya ragu matuƙa.

**Mandu:** To yanzu kina so in…

**Duduwa:** Ka gani ko! Ga shi yanzu ya fara har da alamun fushi sosai. Don Allah ka sa a daina.

**Mandu:** Duduwa, aljanu ne waɗancan, addu'ar ce take kama su. Ki bari mu kammala wannan, ba ƙaramin yaƙi za mu yi da su ba, amma daga ƙarshe za mu yi nasara! Zo mu koma ciki.

**Mai ba da labari:**

Yawancin jama'ar nahiyar Afirka sun yarda da cewa, aljanu ne kawai suke sa mutum ya samu taɓin hankali. Saboda haka addini na taka rawar gani sosai a kan yadda jama'a suke kallon masu taɓin hankali.

Shi kuma John, bayan ya yarda da ya riƙa zuwa ganin Dr. Mudi don ya riƙa samun shawarwari, da kuma fara shan maganin da zai sa ya rage tunani, sai ya ga lokaci ya yi da ya kamata ya koma bakin aikinshi na da. Saboda haka sai ya koma don ya ga tsohon mai gidanshi, wato Mr. Patel.

**Fitowa ta 3: A kanti**

**John:** Barka dai. Kin san kuwa da ni ne kashiyan da yake zaune a kan wannan komfuta? Sunana John.

**Kashiya:** Malam don Allah ka yi haƙuri, aiki ya yi min yawa, ka yi gaba.

**John:** Hmmm, shi ke nan. Shi ke nan, amma zan dawo. Wannan wurina ne. Zan dawo. Ki dai ci gaba da riƙe min kujerata, kin ji?

**Kashiya:** Kai mahaukaci ne? ... Don Allah ka ɗan yi min haƙuri Malam. Bari in yi waya saboda wannan mahaukacin mutumin.

**John:** A'a, ba sai kin buga wayar ba, ai ofishin Patel ɗin zan je. Kuma na san cewa ma yanzu ya ganina a cikin kyamarar da ke ɓoye. Aha, ba na gaya miki ba, ga shi can ma yana zuwa.

**Patel:** John, abin mamaki! Don Allah zo mu je office ɗina.

**John:** Barka da warhaka Mr. Patel! Na dawo!

**Patel:** Na lura da haka, lallai na lura da haka. Shigo ciki, shigo ciki mana. … Me kake yi haka? An ce min ka samu taɓin hankali, amma ban san cewa al'amarin ya kai haka ba. Har barazana kake yi wa ma'aikatana?

**John:** Ina! A'a, Mr. Patel, ka ƙara yin kuskure. Na farko dai, ba wani taɓin hankali da ya same ni. Na shiga halin tunani ne kawai da takaici, mummunan takaicin, har ya kai ga saura kaɗan in… amm… ka dai gane… in kashe kaina.

**Patel:** *Om shanti shanti shanti!*

**John:** Mr. Patel, da ma kana fatan a ce na mutu a yarenka?

**Patel:** A'a, waɗannan kalaman na nufin ne "hankali kwance, jiki kwance". Ya kamata ka fara wani wasan motsa jiki. Zai yi maka kyau, zai ma zuciyarka kyau. Zai taimake ka sosai.

**John:** Wasan motsa jiki!? Wace magana kake yi? Na zo nan ne don ka dawo min da aikina. Ba wai na zo maganar motsa jiki ba ne.

**Patel:** Kai wani iri ne! Tsaya ka ji John, ka yi haƙuri, amma ba zan iya dawowa da kai aiki ba.

**John:** Mr. Patel, wannan shi ne karo na biyu da ka nuna min rashin kyautatawa. Na farko da ka kore ni daga aiki ba tare da wani dalili ba, sai kuma yanzu, saboda rashin lafiyata. Ina karɓar magunguna yanzu, kuma na fara karɓar shawarwari a kan yadda zan tafiyar da tunanina. Yanzu na fara samun lafiya, na yarda da haka sosai. Idan kuma na

samu lafiya sosai, sai na tabbatar da cewa ka fuskanci hukuma saboda cin zaluna da ka yi.

**Patel:** Barazana ba za ta kai ka ko'ina ba John. Ka je cibiyar kula da masu taɓin hankali ko kuma ka shigo cikin irin addinina. Zai taimake ka. Ka yi haƙuri, ni yanzu ina da aiki mai yawa a gabana. Kuma don Allah kar ka ƙara damun ma'aikatana. Idan kuma ka ƙara, to zan kira maka 'yan sanda.

**John:** Ba mu gama wannan maganar ba, Patel, ba mu gama ta ba!

**Mai ba da labari:**
Wani abu mai wuya da ke faruwa da mutane masu taɓin hankali ko da sun samu sauƙi shi ne, yadda jama'a za su ƙara rungumar su a matsayin mutane masu hankali. A lokacin da yake barin shagon da yake aiki da, su kuma Dije da Amina sun kama hanyarsu ta zuwa ganin Dr. Mudi a asibiti.

**Fitowa ta 4: A asibiti**

**Likita:** Yauwa, na gaba ya shigo! ... To 'yammata, me ke tafe da ku? ... Ku tsaya mana! Ku yi magana ɗaya bayan ɗaya. Amma ke kuwa ba mu taɓa haduwa da ke ba? Ke siririyar nan, da ke nake.

**Amina:** Mun taɓa? Ban sani ba. Wataƙila.

**Dije:** Sunana Dije, wannan ƙawata ce Amina. Kwarai kun taɓa haɗuwa. Ta taɓa zuwa nan lokacin da ta fara jin wasu irin muryoyi. Yanzu kuma abin ya ƙazanta.

**Likita:** Mhm! Kwarai kuwa! Ai har na ce mata ta dawo, amma ba ta dawo ba. Na tabbatar cewa matsalar ta ƙaru tun daga lokacin zuwa yanzu. Faɗa min me ya faru. Saboda yadda na gan ta yanzu, ba ta yi kama da mai taɓin hankali ba. Ga shi ta yi ƙwalliya, ga tsafta a jikinta, kuma kamar ana kulawa da ita sosai.

**Dije:** Ni ce na mai da ita hak, Likita. Saboda yau ta zo wurina ko kaya babu a jikinta.

**Likita:** Mhm…

**Mai gabatarwa:**
Da haka kuma muka kammala shirinmu na yau. Yanzu Amina ta gane cewa tana iya kamuwa da ciwon hauka murarun, wata cuta da ke da wuyan sha'ani, wadda kuma tana da alamomi da yawa da kuma abubuwa da yawa da ke kawo ta. Shin Dr. Mudi zai iya taimakonta ta yaƙi wannan cuta? Shi kuma John fa zai ƙara samun aikinshi na da? Shi kuma Musa zai sami lafiya kuwa?
Duk za ku ji amsoshin waɗannan tambayoyi a cikin shirinmu na gaba. Kafin nan kuna iya ƙara sauraron wannan shirin ta adireshinmu na na yanar gizo, wato dw.de/lbe. Ko kuma ku buɗe shafinmu na Facebook domin yin muhawara a kan shirin. Sai mun sadu a shiri na gaba. Ku huta lafiya.